**SABABAN KARKACEWA INGATACCIYAR AƘIDA DA HANYOYIN RIGAFI DAGA AFKA MUSU**

**Na farko : Dalilan jirkicewa ingantaciyyar aƙida :**

1- **Jahiltar ingatacciyar Aƙida:** Sakamakon bijerewa koyanta da koyar da ita, ko ƙaranci kulawa da himmatuwa da ita; ta yadda ake wayar gari al`umma mai zuwa bata san wannan aƙidar ba, ba ta kuma san abin da yake kishiyantar ta da saɓa mata ba, sai a wayi gari suna ƙudurce gaskiya a matsayin ƙarya, ƙarya kuma a matsayin gaskiya, kamar yadda Umar ɗan khaɗɗabi Allah ya ƙara yarda dashi Ya ce: "Yadda al'amarin yake; za a riƙa warware Hukunci hukuncen musulunci ɗaya bayan ɗaya har sai ya zamanto wanda ya taso cikin Musulunci bai san(zamanin) jahiliyya ba".

Ƙarin bayani game da hadisin: Ana nufin (Bai san Shiribicin da ƴan zamanin jahilyya suka yi ba na shirka da jahilci da wauta da kuma irin rawar da musulunci ya taka har yayi tasiri wajen kawar da shirka da munanan aƙidun jahiliyya).

2- **Bin masu da`awa zuwa ga ɓarna da shuwagabannin ɓata**.

Dalilai game da haka sune :

a- FaɗinSa ﷻ :

﴿ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ أَئِمَّةٗ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلنَّارِۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ لَا يُنصَرُونَ ﴾ القصص: ٤١

"Kuma muka mayar dasu shuwagabanni masu kira zuwa ga wuta; ranar Alƙiyama kuma ba za a taimakesu ba"{ƙasas:41}.

b- Daga Huzaifa ɗan Al-yamani ؓ Ya ce: Manzon Allah (ﷺ) Ya ce : "Masu kira za su kasance a ƙofofin jahannama, wanda ya amsa musu zuwa gare ta, zasu jefa shi acikinta, sai nace: Ya ma`aikin Allah sifanta mana su. Sai Manzon Allah Ya ce: su mutane ne masu irin fatarmu , suna Magana da harshenmu" Muslim ne ya fitar da hadisin.

c- Daga Saubaan ؓ Ya ce: Manzon Allah (ﷺ) Ya ce: " Haƙiƙa abin da nake ji wa al`ummata tsoro: Jagorori ɓatattu". (Ahmad da Tirmizi ne suka fitar da hadisin, Ahmad ne ya inganta shi).

d- Daga Abdullahi ɗan Amri ɗan Aaas, ؓ Ya ce: "Naji Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gareshi yana cewa: "Lallai Allah ba ya ɗauke ilimi lokaci guda, ta hanyar zareshi daga cikin bayi, sai dai yana ɗauke

ilimi ne ta hanyar da ɗauke malamai, har sai yayi saura babu wani malami (masanin Allah) sai mutane su riƙi shuwagabanni jahilai, sai a tambaye su, sai su bayar da fatawa ba tare da ilimi ba, sai su ɓata, kuma su ɓatar". (Bukhari da Muslim ne suka fitar da hadisin).

**Muhimmiyar fa`ida : Masu kira zuwa ga ɓarna :**

Tun a da can da yanzu, masu kira zuwa ga ɓarna da jagororin ɓata su ke kange mutane su hanasu bin hanyar Allah madaidaiciya da kuma Addinin Allah miƙaƙƙe.

**Daga cikinsu akwai:**

- (Samiri) : Samiri mutum ne daga cikin mutanen da suke bautar Saniya, maƙwabtan banu isra`ila. An ce ya kasance cikin mutanen zamanin Annabi Musa Amincin Allah ya ƙara tabbata a gareshi; yayin da Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَامُ ya tafi ganawa da Ubangijinsa akan dutsen ɗuur, sai samiri ya sassaƙawa banu isra`ila ɗan maraƙi na zinare; kuma ya raya (ƙawata) musu cewa Ubangijinsu ne kuma Ubangijin Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَامُ, kuma shi wannan ɗan maraƙin na zinare wani sauti ya kasance yana fita daga gareshi kamar sautin Saniya (yana kuka irin na ɗan maraƙi); ana cewa wannan sautin (khuwaar); hakan kuwa ya faru ne sakamakon iskar da take fita daga cikinsa, su kuma banu isra`ila sun kasance idan suka ga haka suna suna kewaye shi suna rawa, suna farin ciki .

  Shi ne wanda ya ɓatar da mutanen Annabi Musa عَلَيْهِ السَّلَامُ daga bautar Ubangiji Allah M, kuma ya ƙawata musu bautar ɗan mariƙi da barin bautar Allah, kamar yadda Allah ﷻ Ya ce game da sha`aninsa:

﴿ قَالَ فَإِنَّا قَدْ فَتَنَّا قَوْمَكَ مِنْ بَعْدِكَ وَأَضَلَّهُمُ ٱلسَّامِرِيُّ ﴾ طه: ٨٥

"(Allah) Ya ce: To lalle mun jarrabi mutanenka a bayanka, samiri kuma ya ɓatar dasu". {Ɗaha: 85}

- Daga cikinsu akwai: (Amru ɗan Amir Al-khuza`iyyu). Daga Nana Aisha رَضِيَ اللَّهُ عَنْهَا tace : Manzon Allah tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gareshi Ya ce: " Na ga wutar jahannama sashinta yana bugun sashi, naga Amru yana jan hanjinsa (acikinta), shine farkon wanda ya `yanta taguwa da nufin bakance ga gumaka". (Bukhari da Muslim ne suka fitar da hadisin).

Ma`anar (Sayyabas- Sawaa`ib): Yana nufin shine wanda ya bar taguwa ta tafi kamar yadda ta ke so; ba tare da an hau kan ta ba, kuma ba a kange mata mashayar ruwa da gurin kiwo ba, hakan bakance ne da yake yi don neman kusanci da gumaka.

Shi yasa Annabi (ﷺ) yaganshi yana jan hanjinsa a wutar jahannama, saboda shine farkon wanda ya canja addini annabi Isma`il; ya kafe gumaka ( Ana bauta musu) , saboda shine ya 'yanta taguwar bakance.

**A zamanin yanzu : Masu zurfafawar rafidawa:**

Sun saɓawa ginshiƙan Ahlussunnah a al`amura masu yawa, daga ciki akwai:

- Suna mayar (Ƙin karɓar) da ingatattun hadisan Annabi sallallahu, ko kuma inkarin su saboda son rai da son zuciya, ba tare da bin ƙa`idojijin ilimin hadisi da malaman hadisi su ka tafi akan ta ba, daga cikin abin da su ke yi ƙyamatarsu (inkarinsu) ingattatun hadisai da bayanansu ya zo daga gurin Annabi (ﷺ) game da wasu al`amuran gaibu na alƙiyama da alamominta wanda za su kasance a ƙarshen zamani; kamar yadda yake a al`amarin (Dujal) da (Saukowar Annabi Isa عَلَيْهِ السَّلَامُ) da kuma (Mahdi) رَضِيَ اللَّهُ عَنْهُ
- Mahdi Allah ya yarda dashi shine : Muhammad ɗan Abdullahi Al-Alawiyyu Al-Faɗimiyyu Al-Hasaniyyu Allah ya yarda da shi , Allah zai shirya shi a cikin yini; ma`ana zai karɓi tubansa, kuma ya datar dashi, ya fahimtar da shi, kuma ya shiryar dashi alhali kafin lokacin ba hakan yake ba. Kuma Allah zai ƙarfafe shi da wasu mutane daga mutanen gabas su taimaka masa, su kuma tabbatar da ƙarfin shugabancinsa, shine wanda aka yaba akayi alkawarin zuwansa a karshen Zamani, za ayi masa mubaya`a awajen ɗakin Allah ya zama khalifan musulmai.

**Muhimmiyar fa`ida:**

Anan ba ana nufin Mahdin da rafidawa suke nufi ba: Cewa yana nan a yanzu suna jiran fitowarsa daga Sirdabin Samura`a (Sunan guri ne da rafidawa suke raya cewa mahdinsu yana gurin zai fito ); wannan kuwa nau`i ne na sambatu da kuma kufcewar hankali me tsanina da yazo musu daga shaiɗan. Domin babu wani dalili daga alƙur`ani da hadisi ko nagartaccen hankali da yake tabbatar da hakan .

- Sukar da rafidawa ke yi wa sahabban manzon Allah amincin Allah ya ƙara tabbata a garesu; musamman akan sahabi mai girma: Mu`awiya ɗan abi Sufyan ﷺ da suke ƙaga masa cewa: (Shine farkon musibarmu)!!
- Zurfafawarsu (Wuce gona da iri) wajen girmama hankali (Kambama hankali ), da ɗaga shi sama da matsayin da ya dace dashi; ta yadda suka sanya shi mai hukunta nassoshi na al`ur`ani da ingatacciyar sunna; kuma su ka sanya (hankali) jagaba akan nassi.

Daga cikin dalilan da suke sanyawa a jirkicewa ingatacciyar aƙidah akwai:

3- **Biyewa son zuciya:** Shine bin abin da take so da kwaɗayinsa, wanda zai iya zama mai amfani gare ta ko kuma mai cutarwa a tattare da ita, abin da ake nufi anan shine abin da zai cutar da ita, da zai fitar da ita daga cikin gaskiya. Dalilai game da haka sune:

a- FaɗinSa ﷻ :

﴿ أَفَرَءَيْتَ مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَىٰهُ وَأَضَلَّهُ ٱللَّهُ عَلَىٰ عِلْمٍ وَخَتَمَ عَلَىٰ سَمْعِهِۦ وَقَلْبِهِۦ وَجَعَلَ عَلَىٰ بَصَرِهِۦ غِشَٰوَةً فَمَن يَهْدِيهِ مِنۢ بَعْدِ ٱللَّهِ ۚ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ﴾ الجاثية: ٢٣

" Shin kuwa ka ga wanda ya ɗauki son zuciyarsa (shine) abin bautarsa, Allah kuwa ya ɓatar dashi akan yana sane, ya kuma rufe jinsa da ganinsa, to wane ne zai shiryar dashi idan ba Allah ba? me yasa bakwa wa`azantuwa" .{Jasiya:23}.

b- FaɗinSa ﷻ :

﴿ فَإِن لَّمْ يَسْتَجِيبُوا۟ لَكَ فَٱعْلَمْ أَنَّمَا يَتَّبِعُونَ أَهْوَآءَهُمْ ۚ وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيْرِ هُدًى مِّنَ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴾ القصص: ٥٠

"To idan basu amsa maka ba, sai ka sani cewa ba abin da suke bi sai soye-soyen ransu kawai. Babu wanda kuwa yafi ɓacewa kamar wanda ya bi son ransa ba tare da wata shiriya daga Allah ba, lalle Allah baya shiryar da mutane azzalumai". {Kasas: 50}.

**Muhimmiyar fa`ida :**

4- **Zurfafawa (Wuce gona da iri ) ga bayin Allah na gari :** shine kambamawa wajen yabonsu, da ɗaga su sama da matsayinsu, suna sanya musu wani nau`i na ibada; don neman kusanci ta hanyar yanke-yanken (Dabbobi) da bakance, da sadaukar da abin yanka, da addu`a, da neman agaji da neman albarkatu a makwantansu ( ƙabarburansu), kamar yadda ya faru ga mutanen Annabi Nuhu ﵇ da nagartattun cikinsu yayin da su kace masa:

﴿ وَقَالُواْ لَا تَذَرُنَّ ءَالِهَتَكُمۡ وَلَا تَذَرُنَّ وَدّٗا وَلَا سُوَاعٗا وَلَا يَغُوثَ وَيَعُوقَ وَنَسۡرٗا ﴾ نوح: ٢٣

" Su ka kuma ce: Kada ku bar abubuwan bautarku, kuma kada ku bar waddu da suwa`u da yagusu da ya`uku da nasaru". {Nuh:23}.

Kamar kuma yadda muke ganin yanzu yana faruwa a wajen masu bautar ƙaburbura a garuruwa da dama.

Daga cikin dalilan da yake nunu da haramcin hakan :

a- FaɗinSa ﷻ :

﴿ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا تَغۡلُواْ فِي دِينِكُمۡ وَلَا تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ إِلَّا ٱلۡحَقَّۚ ﴾ النساء: ١٧١

"Ya ku ma`abota littafi, kada ku wuce iyaka cikin Addininku, kuma kada ku faɗi wata magana game da Allah sai ta gaskiya". {nisa`i: 171}.

b- Faɗin Manzon Allah (ﷺ): "Ya ku mutane, ina gargaɗinku game da zurfafawa (wuce gona da iri) acikin addini, domin abin da ya halakar da waɗanda su ka kasance gabaninku shine zurfafawa (wuce gona da iri ) acikin Addini". (Ahmad da Nisa`i ne suka fitar da hadisin, Albani ya inganta shi) .

**5- Makahon kwaikwayo**

Shine biyayya ga iyaye da malamai da shuwagabanni da manya, makauniyar biyayya ba tare da wani dalili ba ko hujja ba. Dalilai masu yawa sun zo akan haka; daga ciki akwai:

a- FaɗinSa ﷺ :

﴿ بَلۡ قَالُوٓاْ إِنَّا وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّهۡتَدُونَ ﴾ الزخرف: ٢٢

" A`a cewa dai suka yi: Lalle mu mun sami iyayenmu akan wani addini ne, mu kuma lalle sawunsu mu ke bi". { zukhruf: 22}.